# GUDUMUWAR MALAMAI GA YADA ADDININ MUSULUNCI A KASAR HAUSA


DAGA

**SHEIKH MUHAMMAD ISA TALATA MAFARA**

**CIBIYAR NAZARIN MUSULUNCI**

**GWIWA LOW-COST, SOKOTO**


MAKALAR BAKO MAI JAWABI WAJEN TARON KARAWA JUNA SANI NA MALAMAI WANDA MAJALISAR SARKIN MUSULMI TA SHIRYA DOMIN CIKA SHEKARU DARI BIYU DA KAFUWAR DAULAR USMANIYYA WANDA AKA YI A CIBIYAR NAZARIN ALKUR'ANI TA ATTAHIRU DALHATU BAFARAWA, SAKKWATO, DAGA 23-25 GA WATAN YULI, 2004

*Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jinƙai*

## GUDUNMUWAR MALAMAI GA YADA ADDININ MUSULUNCI A KASAR HAUSA

### GABATARWA

Abu ne sananne cewa Musulunci shi ne addinin da Allah ba zai karɓi wani addini daga kowa ba a ranar Alƙiyama face shi. Haka kuma Musulunci shi ne addinin da dukan Manzanni suka yi kira zuwa gare shi tun daga Annabi Nuhu har zuwa ga Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Allah na cewa "Kuma wanda ya nemi wanin Musulunci ya zama addini, to, ba za'a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lahira yana daga cikin masu hasara." (3:85)

Allah kuma ya fada:

"Ya shar'anta muku, game da addini, abin da ya yi wasiyya da shi ga Nuhu da abin da Muka yi wahayi da shi zuwa gare ka, da abin da Muka yi wasiyya da shi ga Ibrahim da Musa da Isa, cewa ku tsayar da addini sosai, kuma kada ku rarrabu a cikinsa." (42:13).

Bayan da Manzo ya yi wafati sai Sahabbai suka tsayu da sadar da wanann addini zuwa ga al'umma da jagorancin Halifofi shiryayyu.

Bayan wucewarsu sai Malamai suka ɗauki wannan nauyi, domin su ne magada Annabawa kamar yadda Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya faɗa. Annabawa kuwa kamar yadda aka sani ba dukiya suka bari ba, a'a sun bar ilmi ne. To, tun a wancan lokaci malamai suka tsayu da wannan aiki na shiryar da al'umma ga al'amarin duniyarsu da lahirarsu. Malamai sun yi haka a kowane zamani kuma da kowane wuri. Abu ne

sananne cewa Musulunci ya shigo a Afirka a zamanin Halifa Umar ɗan Haɗɗabi a lokacin da Amru ɗan Asi ya ci Misra da yaƙi.

Daga baya kuma yake-yake na cin nasara suka yawaita a Afrika ta Arewa a hannun Ukubatu ɗan Nafi'u. Daga can ne Larabawa 'yan kasuwa suka shigar da Musulunci a Afirka ta Yamma. A dalilin haka aka sami dauloli na Musulunci a cikinta. Wannan kamar a Ghana da Mali da Sungai da sauransu. Daga baya kuma aka sami kafuwar Daular Musulunci a hannun Shehu Ɗanfodiyo. Wannan kuwa a ƙarni na sha takwas zuwa na sha tara ga miladi wanda ya yi daidai da karni na sha biyu zuwa na sha uku ga hijirar Manzo tsira da amincin Allah su tabbat a gare shi.

TARIHIN WASU DAGA MASHAHURAN MALAMAI DA SUKA YAƊA ADDINI A KASAR HAUSA

Kasancewar ana magana ne a game da malamai da ƙoƙarinsu a wajen yaɗa addini a ƙasar Hausa, to, yana da kyau mu ambaci wasu daga cikinsu. Wannan domin a sansu a kuma san gudunmuwar da suka bayar. Abin da ke tafe a nan wani ɗan ɗosane ne dangane da abin da Sarkin Musulmi Muhammad Bello ya ambata a cikin littafinsa na Infaƙu kuma da abin da Malam Adamu Abdullahi Ilori ya ambata a cikin littafinsa na Il-Islam Fi Nijeriya. Daga waɗannan malamai akwai:

1. Abdullahi Suka wanda yake Bafillatani ne daga Katsina. Ya kasance shahararren malamin da babu kamarsa a nasa lokaci. Ya yi karatu a Agdas da Fazzan, sa'annan ya koma Katsina domin cigaba da koyarwa har Allah ya yi masa rasuwa a can. An ce shi ne farkon Malamin da ya nakalci littafan nan na hadisai ingantattu guda shida. Ya wallafa ƙasidarsa mai suna "Adiyyatul-Mu'di" wadda ke ƙunshe da baitoci dubu da ɗari biyar.

2. Daga cikinsu akwai malamin nan mashahuri wanda aka sani da Dan Marina. Wannan malami yana dà littafi a kan sharhin Ishiriniya ta Alfazazi. Shi ma mutumen Katsina ne.

3. Haka kuma akwai wani malami daga Katsina mai suna Muhammad Ɗanmasani. Wannan malami ya wallafa littafai da yawa. Daga cikinsu akwai "ANNAFHATUL-AMBARIYYA" sharhi ne na Ishiriniya, haka kuma akwai "BUZUGUS-SHAMSIYYA" sharhi ne na Ishimawi; haka kuma yana da "AZHARUR-RUBA FI AKHBARI BILAD YARÙBA." Shi ɗan makaranta ne ga Malam Ɗanmarina.

4. Sai kuma Malam Haruna daga Zariya wanda yake Bafillatani ne, amma sun ce asalinsa daga Fazzan ne. Ya zauna a ƙasar Zamfara, yana da littafai da ƙasidai. Wannan kamar ƙasidarsa akan masu riwaya na littafan Buhari. Haka kuma da wata ƙasida tasa a kan zargin shagaltuwa da ilmin taurari.

5. Daga cikinsu akwai sananne malamin nan Umar ɗan Muhammad Attarwadi. Shi wannan malami marubuci ne, kuma yana da ƙasidodi na waƙe. Daga littafansa akwai abin da ya rubuta zuwa ga wani daga cikin 'yan'uwa yana yi masu bayanin waɗansu littafai da ba su kamata a shagaltu da karatunsu ba. Waɗannan littafai sun kai sama da hamsin. Ya ce "saboda mafi yawan abin da ke cikinsu mai rauni ne kuma ɓarna ne, haka hadisan da ke ciki maulu'ai ne."

6. Daga cikinsu akwai malami, mashahuri mai bincike, mai albarka, watau Jibrilu ɗan Umar Shehu Usman ya ambata a game da shi a cikin littafinsa na "Shifa'ul-Aalil" cewa: "Ya kamata mutanen wannan ƙasa ta Sudan su san sashin abin da Allah Ya ni'imta a kansu, domin su yi ƙoƙari ga gode masa kuma su sami ƙari dangane

da samuwar wannan malami a cikin wannan kasa" sai Shehu Usman ya ambata wasu daga darajojinsa. Daga cikinsu akwai.

A. Shi ne farkon wanda ya ɗauki tutar ilmi kuma ya watsa shi; haka kuma ya sami ɗaukakar ziyartar ɗakin Allah da yin hajji a gare shi kuma da ziyarar Manzo a Madina har sau biyu.

B. Ya kai matuƙa ga shagaltuwa da Alƙur'ani da sunnar Manzo; kuma da kwaɗaitar da mutane zuwa ga haka.

C. Shi ne wanda ya fara rosa miyagun al'adun a wannan ƙasa, Shehu ya ce: sai abin daga baya ya kammala a hannunsu.

D. Ya kai matuka ga ibada da kishi ga musulunci, kuma shi mai halaye ne nagari. A game da shi Shehu Usmanu ke cewa: "Duk wani abu da aka faɗa game da ni, to, ban kasance ba face kunfa daga kunfan Jibrilu."

A game da shi Malam Abdullahi Dan Fodiyo ke cewa:

"Jibrilu wanda ta hanyarsa ne Allah ya ɗora addini madaidaici kuma mai miƙaƙƙen tafarki.

"Rana ce ta hantsi da ta ɓullo daga yamma ta nufi gabas tana mai haske ga Kuraishawa da mutanen Madina."

A dangane da shi Sarkin Musulmi Bello ke faɗa:

"Malamin malamai a ƙasar mu shi ne Jibrilu, albarkarsa ba'a iya bayaninta.

"Da shi aka kuranye duhu na ɓata, wannan ka ce fitila ce da ta kuranye duhu."

Malam Jibrilu dai yana daga 'yan makarantar mashahurin malamin nan Murtala Zubaidi wanda ya yi wa Ihyau

Ulumid-Dini na Gazali sharhi, kuma wanda yake shi ne mawallafin littafin Tajul-Arusi.

Malama Jibrilu shi ne babban malamin Shehu Usmanu kamar dai yadda muka ga Shehu ya ambaci haka da kansa.

7. Daga cikinsu akwai Malam Kabara daga jikokin mashahurin malami Malam Ahmad Buba mutumen Tumbutu. Wannan malami ya yi karatu a Jami'ar Sankore, kuma sun tara zamani da Jibrilu ɗan Umar da Malam Dahir ɗan Ibrahim. Ya kasance daga bayin Allah kuma daga Waliyyai masu girma. Yana da 'yan makaranta da 'ya'ya da suka kai gaya. Ya rasu a wajajen shekara ta 1844. Daga 'ya'yansa akwai Malama A'isha wadda ke tafsirin Alƙur'ani a gidan Sarkin Kano a cikin watan Ramalan.

8. Daga malaman wannan ƙasa akwai Muhammad ɗan Abdul-Karim wanda aka sani da Malam Magili mutumen Tilmisana. Yana daga manyan malaman karni na tara ga hijira. Ya bar Tilmisana a dalilin wani rikici da ya auku a tsakaninsa da Yahudawa a can. Ya tafi har ya isa Takadah ya zauna a can yana karantarwa. Daga baya ya isa Katsina ya haɗu da Sarkinta. Sa'annan ya zo garin Kano ya koyar a nan. Har ya zama shi ne Alkali kuma mai ba da fatawa a cikinta. Daga baya kuma ya je a Sungai a lokacin da Askiya Muhammad ke sarauta kuma ya riƙe shi malaminsa na fatawa. Magili ya hadu da mashahurin malamin nan na Misra watau Suyudi ko dai a Katsina ko a Takadah ko kuwa a Tumbutu suka tattauna a game da ilmin Manɗiƙi. Shi Magili yana ganin halacin ilmin; a lokacin da Suyuɗi ke ganin haramcinsa. Magili ya rasu a garin Tuwat a shekara ta 909 ga hijira. Allah Ya jikansa. Amin.

Malam Magili a lokacin zamansa Kano ya rubuta wa Sarkin Kano Muhammad Rumfa littafi a game da al'amuran siyasa da mulki da gudanarwa. Wannan littafi ana ɗaukarsa ƙamar tsarin mulki na musulunci na farko a ƙasar Hausa. Malam Abdullahi Ɗanfodiyo ya ciranto maganganu masu yawa daga gare shi a cikin rubuce-rubucensa da ban daban tun ma ba'a ce a cikin littafainsa na Liya'ul-Hukkami ba, wanda shi ma Malam Abdullahi ya wallafa shi a Kano.

Waɗannan malamai da aka ambata a sama da suka gabaci Shehu Usmanu, wadansu kuma suka yi zamani da shi sun yi amfani da duk abin da ke cikin ikonsu a wajen wa'azi da karantar da mutane. Allah ya saka musu da mafificin alherinsa.

## SHEHU USMANU DANFODIYO DA ALMAJIRANSA

Shi ne Shehu Usmanu ɗan Muhammadu Fodiyo Ɗan Usmanu ɗan Salihu wanda aka Haifa a Maratta a shekara ta 1168 wadda ta dace da shekara ta 1754 ga miladi.

Haƙiƙa ya tasa tasawa kyakkyawa, kuma ya sami kyakkyawar tarbiyya daga mahaifansa. Ya tasa da son ilmi da ibada har Allah ya yi masa budi a ciki. Ya yi karatu ga mahaifinsa Fodiyo, haka kuma daga mahaifiyarsa Hawwa'u Kuma da kakarsa Rukayya. Daga baya kuma ya yi karatu ga Usmanu Binduri wanda yake Bakabe ne, haka kuma daga Jibrilu ɗan Umar kuma da Muhammad ɗan Raji da dai sauran malamansa na daga Fulani da Hausawa da Barebari. Duka malamansa 'yan ƙasa ne babu Balarabe a ciki. Wanann wata baiwa ce da Allah ya yi wa wannan bangare na Afirika ta yamma.

## BAIWAR DA ALLAH YA YI WA SHEHU

Malam Adamu Abdullahi Ilori ya ambata a cikin littafinsa da ya gabata cewa, akwai abubuwa masu yawa da Allah ya yi wa Shehu baiwa da su, wadanda wani bai sami irinsu ba, a'a ba a nan a cikin Afrika baƙar fata ba, ko da ga Larabawa ba'a cika samun haka ba. Wannan idan muka lura za mu ga shi ne farkon mai da'awa a Afrika da ya tsayu ga canja munkaran da zuciya, sa'annan da harshe, sa'annan kuma da hannu. Sai kuma daga baya da tara sojoji da daukar makamai tare da kafa daula wadda ke hukunci da Alkur'ani da sunnar Manzo. Wannan a bisa ga yanayin daula ta farko da halifofi shiryayyu suka gudanar.

Shehu bai yi tarewa da wani basarake ko wani mai mulki a wajen kafa daula ba. Wannan ba kamar yadda Abdullahi ɗan Yasin yayi ba da ya nemi taimakon Sarki Yahya ɗan Ibrahim da Abubakar ɗan Umar a wajen kafa daular Murabiduna. Haka kuma ba kamar yadda Muhammad ɗan Abdul-Wahhabi ya yi ba da ya nemi taimakon basarake na Saudi a wajen kafa daular Saudiyya ba. Haka harwayau bai yi da'awa irin ta Faɗimiyya ko Mahdiyya ba kamar yadda Muhammad ɗan Tomarta ya aikata ba a wajen assasa daular Muwahhidina can Magrib, ko kuwa yadda Ahmad Al-Mahdi ya yi a wajen asassa daularsa a can Sudan ba.

Za mu ga kuwa Danfodiyo ya yi tarewa da malamai masana Fikihu a wajen daidaita al'ummarsa da alkalaminsa ta hanyar rubuta littafai masu tarin yawa a fannoni daban daban na daga ibada da siyasa da cigaban al'umma da sauransu. An sami kamar malamai guda ɗari da makarantarsa ta yaye kuma kowanensu ya kai matsayi na Mujtahidi a cikin mazhaba ta Malik.

Haka Shehu Usmanu ya yi tarewa da malaman sufanci a wajen tarbiyyar rayuwa da zikirori da wuridda. Wannan kuwa a kan darikarsa ta kadiriyya

wadda salsala tasa kẹ da dangantaka da Muhtarul-Kunti a wajen wuridi da Ahlul-Baiti.

Sa'annan Danfodiyo ya yi tarewa da masu jihadi a kan hanya ta Allah. Ta haka ya ɗauki makami, ya jagoranci rundunonin yaki, ya yi jihadi har ya sanya kalmar Allah ita ce maɗaukakiya, kalmar kafirci kuma makaskanciya.

Da wannan ya assasa daula ta musulunci wadda fadinta ya game dukan sashin da ake cewa Arewacin Nijeriya a halin yanzu, kuma da wani sashi a cikin Jamhuriyar Nijar da Kamaru.

A gaba ɗaya ana iya cewa Shehu Usman Malami ne kuma Fakihi, haka kuma mai wa'azi kuma mai tarbiyya kuma mujaddadi, shugaba, jagora, kuma limami haka kuma basarake kai ya ma zama al'umma gaba ɗaya.

Daga wadanda suka taimakawa Shehu a wajen wannan aiki na watsa musulunci akwai ƙanensa kuma shakikinsa Malam Abdullahi. Shi Malam Abdullahi ya yi karatu daga mahaifinsa haka kuma ya yi daga yayansa Shehu Usmanu, haka har wayau ya yi karatu daga malamai masu yawa na zamaninsa; wannan har ya zama masani ga fannoni masu yawa na ilmi abin da ya kai malaman zamaninsa na yi masa lakabi da "Nadiratuz-Zamani," watau abin da ba'a cika samun kamarsa ba ga lokaci. Ya wallafa littafai da suka haura ɗari biyu a kan fannoni daban daban. Mashahurai daga cikinsu su ne "Alfiyatul-Usul" da "Al-Bahru Al-Muhiɗi" da "Al-Hisnu al-Rasin" haka kuma da 'Liya'ut-Tawil" Allah ya yi wa Malam Abdullahi rasuwa a shekara ta 1245.

Daga waɗanda suke ba da gudunmuwa ga Shehu a wajen watsa musulunci akwai ɗansa Sarkin Musulmi Muhammad Bello. Shi ma kamar Abdullahi ya yi karatu ga Shehu haka kuma ya yi ga Malam Abdullahi. Allah ya yi masa baiwa da fahimta kuma ya tara ilmi mai dimbin yawa abin da ya kai shi ga wallafa littafi a kan fannoni daban daban. Littafinsa na Infakul-Maisur ba a

ɓoye yake ba, kuma shi wannan littafi shi ne ginshiki kuma taska ga duk mai bincike ga tarihin wannan ƙasa.

Daga cikin waɗanda suka ba da gudunmuwa ga watsa addinin Musulunci a wannan ƙasa akwai 'yan makarntar Shehu waɗannan da suka karɓi tutoci daga gare shi suka koma sassansu suka karantar da almajiransu kuma suka yi yaƙi kuma suka tsayar da addinin Allah. Wannan kamar Sulaimanu a can Kano da Musa a Zariya kuma da Yakubu a Bauchi haka kuma da Buba Yero a Gwambe. Waɗansu daga cikinsu su ne, Ibrahim Zaki a Katagum, Sambo Digimsa da ɗan'uwansa Larlima a can Hadeja da dai sauransu. Haka kuma akwai Waziran Shehu da na Bello, wannan kamar Waziri Gidado da ɗansa Abdulkadir da sauransu.

Ba za mu manta harwayau da gudunmuwar da kwamandojin yaƙi suka bayar ba, wanann kamar su Namoda da Aliyu Jedo.

Wannan bincike ba zai kammala ba, ba tare da ambaton gudunmuwar malamai mata ba a wannan ƙasa ta Hausa. Mata da yawa sun nuna ƙasu kwarewa tun ma ba ga karantar da 'yan'uwansu mata ba. Zance ya gabata na Malama A'isha 'yar Malam Kabara daga jikokin Ahmad Baba wadda ke tafsirin Alkur'ani a gidan Sarkin Kano a cikin watan Ramalan.

Daga cikinsu akwai Khadijatul-Kubura 'yar Shehu Usmanu. Tana daga waɗanda suka yi hijira tare da Shehu, kuma tana daga wadanda suka sami tarbiyya gaya daga mahaifinta. Tana da ƙasidodi a game da wa'azi da shiryarwar. Ita ce mahaifiyar malamin nan mashahuri Abdul-Kadir ɗan Al-Mustafa.

Daga cikinsu akwai Faɗima ita ma 'yar Shehu ce. Ita ce matar Sarkin Yaƙi Aliyu Jeɗo. Tana daga mata salihai. Ta wallafa littafai a kan sassa daban daban na ilmi. A bisa ga misali tana da ƙasida a kan falalar salati da ƙasida a kan wa'azi haka kuma da kasida a game da falalar zikiri da dai sauransu.

Daga cikinsu kawai Asma'u 'yar Shehu, haƙiƙa ita malam ce kuma mawallafiya. Ta kasance tana karantar da matan da ke zowa a wajenta daga sassa daban daban a lokacin Maulidi da A'shura. Ta kan tsara waƙoƙi a gare su da suka shafi addini domin sauƙin haddacewa. Wannan da manufar almajiran, su haddace wannan abu kuma su watsa su ga 'yan'uwansu mata idan suka koma garuruwansu.

Daga cikinsu har wayau akwai Maryam 'yar Shehu. Hakika waziri Junaidu ya siffanta ta da cewa ita mai biya ce ga Alƙur'ani da sunnar Manzo, kuma mai umurni ce da alheri kuma mia hani ce daga abin ƙi. Mutane sukan aiak da tambayoyi a gare ta, ba mata ba kawai a'a har maza. Misali ga wannan tambayar da Sarkin Kano Usman Dabo ya aika a gare ta a game da mutanen da ke cirata daga kasar Hausa suna masu nufatar Gabas suna masu cewa bayyanar Mahdi ta kusato. Sai ta ba shi amsa mai gamsarwa a game da haka.

## KAMMALAWA

Daga abin da ya gabata muna iya cewa malamai ne suka tsare wannan addini kuma suka watsa shi tun lokacin da ya shigo a wannen kasa har zuwa bayyanar Shehu Usmanu.

Haka kuma kamar yadda muka gani Shehu Usmanu a nasa lokaci ya yi amfani da wa'azi da gargaɗi da rubuce-rubuce kuma da karantarwa da tarbiyya, to, wannan na nuna muna cewa, babu nasara ga malamai a halin yanzu face sai sun bi wannan hanyar da Shehu ya bi. Wannan kuwa saboda an ce, babu gyaruwa ga ƙarshen wanann al'umma face sai da abin da ya gyara farkonta. A dalilin haka yana wajaba ga malamai da su karanci littafan da Shehu da almajinrasa suka rubuta, domin su gano waccan hanya kuma su watsa ta ga mutane. Wanann tun ma ba'a ce Shehu ya kwaɗaitar da jama'a ga karantun littafansa ba da na Malam Abdullahi kuma da na Muhammad